**Réseau National des Chambres d'Agriculture du Niger**

# Kananan kwari farfaru da ake cema mouche blanche a turance


*Dr Haougui Adamou et Bibata Ali Outani (INRAN), Aïssa Kimba et Patrick Delmas (RECA), Dr Garba Madougou et Salissou Oumarou (DGPV) / 19 mars 2019.*

Yau zamu muku hira kan wani mungun kwari dake banna cikin garake kuma manoma sun sanshi kwarai da gaske,wannan kwarin shine ake cema kananan kwari farfaru da ake cema mouche blanche a turance.

In manoma sun san irin bannar da wannan kananan kwarin farfaru keyin saman tattasey da tomati da tonka,abincin su kenan, to har yanzu basu gano irin cutitikan da suke iya hadasama wanan shipkoki ba.

## Yaya ake gane kananan kwari farfaru da kwarin su ?

Su dai kananan kwari farfaru kamar yadda sunan su ya bayyana kananan kwari kwarai kuma farare wanda suke tashi da zarar an gilgiza ganyen shipkar da suke a kai kuma sai sun koma kan wani ganyen, ko da yaushe kwarin shi na nan kalkashin ganyen shipkoki.



- kwai
- jinjirin kwari
- karamin kwari fari da ya kwonge wato yana iya aifuwa.

Jinjirin karamin kwari karami ne kwarai, baya da kafafu, ba yada fukafukai bayada komai,ana ganinshi ne ta hanyar wasu kananan tambo tambo farfaru ko masara da basu motsi kalkashin ganyen.

Suna iya kasancewa dafifi saman gayen,in sunyi yawa sosai to sun hi yin banna kwarai cikin shipkoki.

## Wacce irin banna ce kananan kwari farfaru ke iya haddawa ?

Kananan kwari farfaru nayin banna kashi biyu :



Da farko dai, kananan kwari farfaru da jinjirin su na tsotsar ganyen shipkoki ne kamar yadda sabro ke tsotsar jinin mutun.
Lokacin da kananan kwari farfaru da jinjirin su suka mamaye gayen shipka kamar yadda kuke gani saman wannan hoton, suna karema shipkar karhi harma su kai ga kashe ta.

Na biyu, Kamar yadda sabro kesa cutar masasara, haka kananan kwari farfaru ke iya sama shipkoki cuta bayan sun apkama ganyen saboda da shine suke rayuwa. Wanan cutar ita ce ake cema (virose). Bata da maganin, babu wani maganin da zai tsirar da shipkar da ta kamu da cutar da kanana kwari farfaru suke haddasawa.

| | |
|---|---|
|  |  |
| Cutar kananan kwari farfaru kan ganyen tumati (viose) | Cutar kananan kwari farfaru saman ganyen tattasey |

## Da wanne irin shipkoki ne kananan kwari farfaru da jinjirin su suke rayuwa ?

- Shipkar tahi amarya kamshi ko kimban bayu, tattasai, tanshi mai zahi, aubergine da tumati. Sune shipkokin da kananan kwari farfaru suka fi so ana kuma iya samun su saman wasu shipkokin ko wanda ake nomawa ko kuma ciyawar banza.

- Bannar da kananan kwari farfaru da jinjiran su keyi tahi tsanani kan tattasey, tashi da aubergine

## Yaya ake gane cewar shipka ta kamu?



Kan shipkar tumati tattasey da tashi, ganyen na murdewa ne sai ya kudidine, kuma sai ya sake kala.

Kan iccen tumati,ganyen sai ya zama kore daga nan kuma sai ya koma ruwan hoda kan shipkokin na tumati wanda suka konge.

## Ta yaya ne cutar ke kama shipkoki?

Lokacin da aka haife su,kananan kwari farfaru basu dauke da cutan. Sai lokacin da suka tsotsi ruwan shipka mai malati ne suke iya sama sauran shipkokin masu lahia.
Saboda shine in shipka ta kamu to ayi gagawar cireta don kar ta zama makafar kanana kwari farfaru,wanda nan gaba zasu sama sauran shipkokin cutar.
Tun fil azal wasu ciyawowi na dauke da cutar misali(sobilabi),ya kamata a cire ciyawar banza daga cikin garka.

In garkar makopcinka ta kamu,kuma bai cire su ba,to kananan kwari farfaru na iya zawwa su apkama shipkokin garkar taku. Babu wani maganin dake kashe cutar ta(virose),ya kamata manoma suyi kokowa tare.

## Da wane lokaci ne kananan kwari farfaru suka soma banna a Nijar?

- Ana samun kananan kwari farfaru ko ina a kasar Nijar, ana samun su a cikin dukan jahohin kasa;Suna rayuwa ne daga watan september zuwa watan November sai kuma daga watan Maris zuwa watan Mayu.
- Da zarar sun samu abinci kuma in lokacin zahi ne,nan da nan suke aihuwa.

## Wane irin hanyoyi ne ya kamata abi don yaki da kananan kwari farfaru?

Manoma ya kamata ku san cewa yaki da kananan kwari farfaru abune mai wuya koda anyi unfani da magugunan kashe miyagun kwari na zamani. Gashi kuma kananan kwari farfaru na iya jurema magugunan kashe miyagun kwari na zamani in anyi unfani dasu sau diyawa. Ya kamata ayi unfani da dubaru masu yawa.



Da farko, ya kamata manomi ya rihe rainon irin shi da sange don kare shi daga kananan kwari farfaru tunda wuri.

Karo na biyu, ya kamata manoma su kula da shipkokin su da kew, musaman ma shipkokin da kananan kwari farfaru ke ci kuma suke ayayafa kamar su (sobilobi). Da zarar manomi ya ga kananan kwari farfaru saman wata ciyawa, to yayi kokarin mizge ta.

Manomi na iya shipka kimban bayu (tahi amariya kamshi) wanda ke jawo kananan kwari farfaru,bayan sati biyu sai ya kashe shipkar.
Lokacin da kananan kwari farfaru suka yi kwayaye saman ganyen kinban bayu, ana iya kashe su tare da jinjirin kwarin tun kahin su kai ga zama uwaye. Kuma sai a sake maimaita shipkar ta kimban bayun,wannan shi ke sa a rabu da kananan kwarin farfarun ba tare da anyi, unfani da magugunan kashe miyagun kwari na zamani ba.

A shekarun baya an sha fama da kananan kwarin farfaru bayan an sake dashe,nan ya kamata ayi unfani da magungunan galgajiya don a rage banner (asa magani sau daya cikin sati).

Duk da maganin galgajiyyar da aka zuba,in bannar bata ja baya ba,ya kamata ayi unfani da wani magani na musaman wanda ya hada sindirai da dama (ACETAMEPRIDE),a kiyaye kaidodin daya kamata abi wajan auna maganin,kuma asa maganin kalkashin ganyen shipkokin.

In kun lura cewar bannar tayi stanani a wasu lokutan ya kamata a sauya shipkar kuma a zabi shipkar da ke jurewa kananan kwari farfaru saboda babu wata riba idan an cigaba da saka magani har hiyye da sau biyu a cikin sati.
Kananan kwarin farfaru zasu kara karhi har su kai ga bijirema maganin wanda zuwa gaba baida wani tasiri a gare su.

Idan kuna bukatar Karin bayani to sai ku tuntubi mashawartan nan na kugiyoyin **RECA** da **CRA** kan **92 24 24 24** (Orange) - **89 97 97 74** (Airtel**) - 84 74 74 74** (Moov) **- 93 32 38 92** (Niger-telecom) ko kuma WhatsApp a kan **92 24 24 24.**

Wanan layoyin dai kungiyoyin **RECA**da **CRA** ne suka tanadar muku su don waye muku kai kan ayyukan ku na noman gandari.